YAYA NA, { Part 1 }

.

Producer Baffah Gatan kd,

.

Wata rana na hau Network Sai naga friend

Request Mai suna Salma,

Banyi Accepted din taba sai da Nayi 4week

Sannan nayi Accepted din ta,

Ko danyi Sai na sauka Ban sake hawaba Sai da

Nayi kwana Biyu

Ina hawa kan kace haka Sai naga Anyi magana,

Salma ce tace Salam Ma'abocin Sanyi?

Sai nace wassalam,

Sai tace man Nayi Adding din Kane don Ina son

Murinka mutinci Ni da kai,

Sai nace mata Okay Bamatsala,

Salma

Amma kina wani gari ne?

Sai tace man Ina Zaria city kai fa?

Sai nace Hmmm Nima Ina Zaria Amma kina

wacce aria ne?

Sai tace Bazan fada maka sunan Unguwarmu ba

Sai Zumincinmu yayi karfi sannan zan fada,

Ina fatan bazaka damu ba?

Sai nace badamuwa hmm hakan ma yana dakyau,

Sai nace mata yanzu an kira Sallar Juma'a bara

naje masallaci,

Muhadu misalin karfe Goma Na dare kinji?

Sai tace to Allah ya kaimu,

Sai nace Amin,

Sai na sauka,

.

Ban daki nanufa naje nayi Wanka nasa kaya Jallabiyya ce fara tas, Ga hula zanna kuma akaina na murza,

Na dau ki dadduma Nafito da niyyar wucewa Masallaci,

Ina zuwa falo

Sai natarar da Salma Kanwata tana kallo

Sai nakashe kayan kallo nace mata 'Yar uwata

Lokacin sallah yayi

Sai tayi dariya tace Yayana kenan ai dama kai

nake jira idan zaka masallaci

Zan bika kasauke ni a kofar gidan su Fa'iza

Kawata

kaga lokacin dazaka dawo nagama abinda zanyi

agidan nasu

kaga Sai kabiya ka daukeni Mudawo gida,

Sai nace oky muje da sauri ta dakko gyalanta

tayafa

Muka wuce Ina zuwa nasauke ta a gidan kawar

tata

ni kuma nayi Masallaci,

.

Mu Ukku ne mahaifanmu suka Haifa Sameera

ce babbar yayarmu Maibi mata Nine Abdul-

Ahad Maibi man itace Ummusalma amma

Munfi kiranta da Salma

Salama da Aunty Sameera Abdul suke kirana

dashi Salma kuma tace man Yaya

Sunan Mahaifinmu Alhaji Bashir Mahaifiyarmu

kuma Fatima

Dukkan 'ya'yan da iyayenmu suka Haifa Muna

son junanmu kuma muna matukar girmama

Iyayenmu

Maifinmu yana daya daga cikin masu sarauta

acikin garin Zaria

Mutane da Abokanin mahaifinmu suna kiransa

da Alhaji bashir Gatan kd,

Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris yana matukar

son Mahaifinmu don Mahaifinmu shike bawa

Sarki shawara,

Mahaifinyarmu haifaffar katsina CE awani

kyauye Mai suna Dandume Watarana mahaifina

yaje Dandume ananne yaga Mamarmu fateema

Harsukayi soyyaya mai karfi Sannan sukayi

Aure,

Sameera ce 'yarsu ta farko nine maibi mata

Maibi mani Itace Salma

Tun daganan Allah bai kara basu Haihuwa ba,

.

Bayan ansakko daga masallaci Salma tadunga jirana

a bakin titi Amma ban dawo ba

tajira tajira amma ba alamuna, hakan yasa ranta

ya 6ace gashi da nisa daga inda take izuwa

gidanmu

hakan yasa ranta ya 6ace sosai Takai awa daya

a gefen titi Sai tasamu wuri ta zauna taita

kirana awaya amma Ban daukaba saboda

Lokacin daza afara sallah nasata a Silent,

Bayan angama sallah Abokina Jabeer ya tareni

muna ta fira dashi

Bayan mungama firarne sannan nakama hanyar

zuwa gidan su kawar Salma saboda nadau

Salma mukoma gida,

Ina zuwa Kofar gidan Sai na hangi Salma a

saman wani da Kali Tadukar dakanta kasa,

Sai naje

Gabanta nadan ta6ata nace Kanwata Nayi maki

laifi amma don Allah kiyi hakuri kitashi mutafi

gida

ko magana batayi man ba tatashi tashige mota

Ina biye da ita Abaya

Muna shiga mota Sai nace mata don Allah kiyi

hakuri sannan nafada mata dalilin dayasa ban

dawo da wuri ba,

Sannan tasaki ranta,

Sai tace Yayana kana son sakani cikin farin ciki,

Sai nayi dariya nace karki damu ai hakki nane

na kula dake kekadai ce Kanwata

Munayi muna fira a haka muka isa gida,

Muna zuwa muka tarar da Daddy da momy da

Aunty Sameera

Suna jiranmu mudawo muci abinci,

Bayan munci Abinci Mungama Mukazo muka

zauna a falo Sai wasa dadariya muke,

Misalin karfe 10:09pm nahau Facebook Sai

nahadu da yarinyar da muka fira dazu a

Network Sai tayi man sallama na bata Amsa

a haka mukaci gaba da fira harmuka shaku

Daga karshe soyayya mai karfi ta kullu

wani lokacin idan nahau Facebook banganta ba

banajin dadi

Itama idan bata ganni ba batajin dadi

Sauka takeyi

Sabida sonda nake mata naba abokaina

labarinta shiyasa suke kirana da Haduwar

Network,

watanmu Shida da haduwarmu da Salma a

network Amma bata bani Lambar taba,

Watarana nahau Facebook Sai naganta a Online

Sai nace mata Give me Ur

Number Baby so that I can Call u

Sai tabani Lamarbta ta Glo

Nima na bata Tawa ta Glo,

Sai na sauka,

Ina zaune Sai naga Salma takirani

Wadda muka hadu a Facebook Ina yin Picking

Sai ta kashe muryarta Sai tace Hello my dear

Sai na Amsa mata

Sai tace man Baffa na gobe Ina Free Ina so

muhadu a Teeje wurin da 'yan mata da Samari

suke Shakatawa don Haka Muhadu acan Misalin

karfe 5:00pm nayamma Nayi Farin ciki sosai

danaji tace muhadu a Teeje gobe

bayan mun gama Waya Nafito falo Sai naga

Kanwata Salma Tana ta Sheka dariya

Sai nace mata Lafiya Sai tace babu komai Sai ta

wuce dakinta,

Daddy da momy da Aunty Sameera da Salma

Sun sanni da Abdul-Ahad

Amma basu sanni da Baffa ba Sim card dina

Hudu Kuma kowanne suna dashi amma Basu da

layina na Glo hakan yasa Kanwata Salma tayi

zuciya tace Bazata bani Lambar Glo dinta

saboda Nace bazan basu Sabon Number sim

card dina na Glo ba,

Gari nawa yewa Salma wadda nakecewa my

dear ta kirani Bayan mungaisa Sai nace mata

Misalin karfe nawama kika ce muhadu a teeje

tace

5:00pm

Bayan mun gama Waya Sai nafara Tunanin

Muryar budurwata tayi kama data Kanwata

Salma

Hmm koda yake Ai nasan ba Kanwata bace

Saboda nasan muryar Kanwata

tunanin Dana Rinka yi a wannan Lokacin,

Misalin karfe 4:50pm Nazo falo natarar da

Kanwata Salma Taci kwalliya after dress tasaka ajikinta gashi buguda kari kayan jajaye ne, gata fara sai tayi kyau kuma kayan sun hauta sosai,

Tana ganina

Sai tace man Yaya na Kayannan

sun man kyau kuwa?

Sai nace mata lalalalala Wlh sunyi maki

kyau Ina zakine haka?

Sai tace Hmm wajen kawayena zani,

Sai nace to a dawo lafiya,

Sai tace man Yaya Da Motar ka zan fita

Ban CE mata A'A ba saboda Bana son 6acin ranta,

Nadau key din motar na bata

Sai tayi tsalle

Tafita,

Gaskiya ne kayan da Salma tasa sun bala'in fito da kyanta,

Bayan salma ta wuce Sai na kwanta akan

doguwar kujerar dake falo

Ina kwance Budurwata Salma wadda muka

hadu a Network ta kirani Cikin Tausassar

murya tace Hello my dear yanzu nashigo Teeje

ban gan kaba

Sai nace mata kiyi hakuri Ganinan zuwa Sai tayi

dariya tace Allah ya kawo man kai nace Ameen,

Da sauri natashi nayi wanka Nasa kananun kaya

Jajaye kalar Wanda kanwata Salma tasa,

A jikin rigata An rubuta Gatan kd,

A jikin Facing carf dina Gatan kd aka rubuta,

Sannan naje nasamu Amir Direban Daddyn mu

nace mai Ya bani makulli motar da Daddy ke

zuwa fada da ita

Amir baiyi man gaddama ba ya dau makulli ya

bani

Jeep ce katuwa na nashiga a jikin motar An

rubuta Shamaki sunan sarautar Abbanmu kenan,

a guje naja motar Ina kan hanyata ta zuwa

Teeje

Sai naga Princess Aisha Diyar Sarkin Zazzau,

Sai

natsaya

bayan mun gaisa

Sai tace man Abdul yanzu

muka hadu da Kanwarka Salma taci wata uwar

kwalliya

Kamar diyar shugaban kasa Na tambaye ta INA

zata tace man wajen kawayenta zata,

Sai nace mata nima haka tace man,

Princess Aisha tace man Abdul Ina zaka?

Sai nace Mata Teeje zani,

Sai tace man Nima danayi

wanka Zanzo Teeje din Sai nace mata Yau ina

kikaje?

Tace man naje Kaduna ne Wani taro da

Maimartaba ya turani

Sai nace mata ok yayi kyau,

Sai tace man zanzo teeje idan nakintsa zan kiraka awaya idan nazo,

Sai

nace mata okay zanjira ki,

Da sauri Fadawa suka bude mata kofa tawuce

nima nawuce,

Ina shiga teeje daidai Inda nayi Parking da

motata Wai gawar da zanyi Sai naga Motata

wadda Kanwata Salma tahau

A zuciyata nace dama Kanwata nan zatazo

Shine tayi man karya tace wajen kawayenta zata

Hmm,Tunanin dayayi yawo a zuciyata kenan,

Sai naciro wayata na kira Salma budurwata

Tana dauka

Sai tace man My dear kazo ne?

Sai

nace mata eh Kina ta wane 6arayi ne?

Sai tace man Ina 6arayin da 'yan Mata da Samari

suke wanka Idan kashigo kakalli Gabas zaka

ganni sanye da Jajayen kaya Table din dake gaba na

a samansa zakaga Gwangwanin Maltina da

madarar holandea

kujerar dake facing dina to kai natana nadar

ma Wannan kujerar kazo kawai kazauna Sai naji

dadi A zuciyata har ina cewa aini Network

alhairi ya kawo man Tunda nahadu da wadda

take sona,

Ina zuwa 6arayin da 'yan mata da Samari suke

wanka Na kalli gabas kamar yadda tace na kalli

6arayin gabas

Kunsan wana gani Dana kalli gabas din?

KANWATA SALMA nagaji da jajayen kaya Kuma

duk ga Abubuwan da tayi man kwatance nan,

Sai muka hada Ido da ita hankalina yayi

matukar tashi sosai,

.

Muhadu a Part 2, gobe,

.

Ina fatan kuna tare dani?